Food and Agriculture Organization of the United Nations

Global Soil Doctors Programme



# la'akari akan jijiyoyi

*Fastar la'akari na 8a*

| | | |
|---|---|---|
| MUHIMMANCI | Kula da ratsa kasar jijiya da kuma habakarsa na iya bayyanar da mahimman alamu da ke nuna tsarin kasa da kuma daidaituwar ta. Kasa mai tsananin hana ratsawar ruwa kamar curarriyar kasa ko laka na hana mikewar jijiya a tsaye da kuma habakar jijiya, sai ta sanya jijiya girma a kwance. Haka na iyakance mata tsotson ruwa da sinadaran habakar shuka, kuma yana rage tasirin taki, da leaching da kuma rage yawan amfani. Rubewa da mutuwar jijiya na iya faruwa ne sakamakon kwari da kuma cututtutuka musamman a kasa mai saurin ajiye ruwa dayawa, da kasar da kalanta ya banbanta sanadiyyar sinadarai da kuma rashin iska | |
| KAYAN AIKI |  shebur  spatular  gilashi mai karawa abu girma | |
| Yanda zaa aiwatar | 1) Haka rami kimanin semtimita 40 bisa 40 bisa 40 (70*70*70 in shukar kamar bishiya ce) ta hayan amfani da wukar fulasta ko shebur kokuma ku ijiyeshi hogen kasar da aka tono in zai yiwu |  © D. Ochoa |
| | 2) Tsaftace saman hogen kasar da aka tono da wukar da lura da jijiya. |  © S.Pioli |
| | 3) Domin cika luran da akeyi, ayi amfani da wukar (shubur) don tsaftace bayanan kasar da aka fallasa na ramin da aka tono tare dayin amfani da gilashin kara girma wurin lura da saiwai. |  © S.Pioli |



GLOBAL SOIL PARTNERSHIP

| | |
|---|---|
| ANFANIN WANNAN HANYAR | Saukin tantancewa da kayan aiki marasa yawa |
| GAZAWAR WANNAN HANYAR | Sai an lura da tsarin jijiyoyi a wurare daban daban domin kwatantatawa da samun gamammen sakamako |
| TAMBOYOYIN DA ZA A AMSA | Shin kasar na barin shukoki su habaka lafiyayyun jijiyoyi? Yaya zurfin da jijiya ke kaiwa a cikin kasar? |

| MISALAN TANTANCEWA | | |
|---|---|---|
| MARA KYAU | MATSAKAITA | MASU KYAU |
| Karancin jijiyoyi masu rai da kuma alamomi masu yawa na matsalolin girma (karkacewa, gajarta ko girma a kance, kaurin jijiya). Karancin saiwar dake zuko taki daga iska a shukoki (irinsu gyada, wake) wannan yanayin na iya faruwa koda a saman kasa. Karancin karmami. | Jijiyoyi da dama, a tsaye, tare da rassa masu yawa da gashin (jijiya) masu tsotso sinadarai. | Jijiyoyi Masu yawa, a tsaye, tare da rassa masu yawa da gashin (jijiya) masu tsotso sinadarai. Jijiyoyina iya girma ba tare da matsalar wani abuba ko matsalan rashin sinadarai sannan kuma zasu shige can chikin kasa. Yawan jijiyoyi masu tsotson taki daga iska a cikin shukan dangin wake. Ga kuma karmami masu yawa. |

[1] https://www.nrcs.usda.gov/Internet/FSE_DOCUMENTS/nrcs142p2_050956.pdf